Citation: Fallou Ngom (PI), Jennifer Yanco, Mustapha Hashim Kurfi, Garba Zakari, Babacar Dieng, Daivi Rodima-Taylor, and Rebecca Shereikis. 2022. "A Poem on the British." http://sites.bu.edu/nehajami/the-four-languages/hausa/hausa-manuscripts/falke-1569-wakar-nasara/.

# Waƙar Nasara

[Page 1]

Bismi l-Lāhi al-Raḥmani al-Raḥīm

Wa ṣallallahu ʿalā Sayyidina Muḥammad wa ālihi wa Saḥbihi wa Sallam

Bismi l-Lāhi nufi zani waƙa	Bisa maƙiya Muhammadu annasara

Muna roƙo ga sarki mai sarauta	Mu samu fita mu bar jama'a nasara

Mutane sun ɗume wasu sun makabta	Yawanci sun zamo jama'a nasara

Ka duba daga nassi har ga sharhi	Biyewa na kafirai balle nasara

Idan Allah Ka nufa za mu tashi	Mu yada wuringa su yi jam'u nasara

Idan Allāhu Ka nufi sai mu zamna	Muna roƙo ka ɓata nufin nasara

Idan mun samu iko munka tashi	Mu yada wargi Ka kai mu Madīna nesa ga annasara

Idan an so idan ba a so a tashi	Zama sun tada wasu maza nasara

Batu ne shehu ya yi shi ba shi tashi	Ƙasagga[1] tana zama mulkin nasara

A kai mu da taulafi Allah ka gyara	Uwa da ɗiya da mata ga nasara

Idan ni dai ka tashi ba ni zamani	Zama wa l-Lāhi ba ni biyat nasara

Cikin biyu sai a zaɓi guda a ɗauka	Wa law tashi wa law a bi annasara

Sarki sun fito sun bar garinsu	Bale moro da kanka ka zam nasara

Maza muke ga mu mata sun rigai mu	Akwai wasu a gazajje kan hadara

Gudum mutuwa da son rai a gare mu	Da kau ƙin qaddara a bi annasara

Ina muka yi da dama da hauni suna	Ku tashi mu sa gabanmu mu tsira tsara

[1] *Kasagga* is the northern dialect for *Wannan ƙasar*. The northern dialect is the Sokoto variety of Hausa, which is spoken in the Sokoto, Zamfara, Kebbi, Gobir, and Kontagora areas, and other parts of the Hausa-speaking regions in the Republic of Niger, including Maradi, Tawa, Niamey and Zinder.

Idan ka ce akwai wahala ga tashi Lahan duka na ga masu biyan nasara

Idan iko ka kai ko ka ƙi tashi Ina iko cikin ikon nasara

Idan sun ba ka kyauta kada ka amsa Dafi na sunka ba guba nasara

Suna foro gare mu bar zalama Mazalunta da kansu ɗiyan nasara

[Page 2]

Baƙar fitna gare su da kau makidah Ta ɓata dinin Musulmi annasara

Halin da mukai ga yau aka bayyanawa Dalili ke ga aka sako nasara

Ku bar jin masu cewa ba'a tashi Ina halin zama ga annasara?

Mu maida gabanmu Mecca mu zo Medina Medina da Mecca dai a ba nasara

Batu na shehu ya yi shi ba shi tashi Saʿā ta ya faɗeta ta annasara

Muna da nufa idan mun samu iko Mu ja daga mu kore annasara

Idan ko sun kashe mu mu sam shahāda Mu zo al-Janna sai mu ishe maƙara

Maza gaba sun ga nassi mun ga dahir Zama yau ga mu ga yankin nasara

Biɗa guzuri ga kowa wajibi na Musulmi kar mu yarda biyan nasara

Mu zan dhikri mu zan kau yin ṣalāti Da adalci mu taushe annasara

Talakka da mai gari duk ɗai garesu Walaƙanci akwai shi ga annasara

Hukumci ya buwaya ga masu iko Ina wada za mu yi mu buwayi nasara

Munafukkai cikinmu yawa garesu Waɗanda ka kyauta al'amarin nasara

Idan Allah taʿālā ya jiƙan mu Shi ba mu mujidaddi mu buwayi nasara

Da masu zuwa cikinsu suna jiyayya Munafukkammu ke ga nasara

Musulmi masu ƙin fara'a garesu Waɗannan sun zamo bikon nasara

Musulmi in musība ta matsanta Ku roƙi ubangijinku hawuya annasara

Da mai cewa abinsu shina da kyawu Ku bar sa ku sa shi cikin annasara

Da mai zina sai mu soma kafiri na Dan bai tuba ya zama annasara

Da mai cin dukiyar wani babu ḥujja Ku bari ai sai kusa shi cikin nasara

[Page 3]

Da mai gama ƴan uwa don su yi ƙiyayya Shi bar cewa a kai wa nasara

Da mai majigi ko kuwa shiga hanya Muna nan zaman tare da su annasara

Azan ʿidda a bar amre da ʿidda Mu yi lura mu bar aikin nasara

Tsaron waqti ga ṣalla wājibī na Mu bar ja nai mu bar yi tun da saura

Saraki kar a maida talakka bawa A bauta sai awa bautan nasara

Nasara fari gare su bisa jikinsu Cikinsu baƙi ƙirin shi kan nasara

Akwai wasu baya gashi a garesu Baƙin halinsu ya fi a annasara

Sāʿata ta kusata ta al-Qiyāma Sharuɗa mun ga dai don ga nasara

Akwai Yajuju ba ya da ta su illa Sukan cika duniya su fa hi nasara

Akwai mu da magani mu tsaya ga Allah Garai muka dogara mu ba wai nasara

Idan kuwa an ƙiya ina da ḥujjah Ina ga ubangijina mai nasara

Zama al-Janna babu ta duk ga bawa Balle shi hana shi sani cikin saʿīra

Ga Allah zan biɗatta ga al-Rasūlu Gama shi anka ba ceto mu tsira

Ka samu cika da imanimmu Allah Akwai wata firgita bai cin nasara

Da ran mutuwa da ran tashin Qiyama Da wanga ga taliki mai annasara

Daɗa al-ḥamdu na cika wagga waƙa Da ikon wanda ya yi mu yai nasara

Tammat